# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Bitrus da Ikon Addu'a



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

Manzo Bitrus ya
yi tafiya ko’ina
a kasar yana
gaya wa kowa
da kowa
game da
Yesu.

Wata rana, a wani gari
mai suna Lidda, ya sadu
da wani mutum wanda
yana kwanciya a gado,
babu tafiya, har shekaru
takwas. “Yesu Kiristi ya
warkar da kai,” Bitrus
ya ce. “Tashi ka gyara
gadonka.” Sai mutumin
ya tashi nan take.
Mutanen da suka ga

wannan
suka juya ga
Ubangiji.



**Kusa da wurin a garin Joffa, mutane suna cikin bakin ciki. Wata mace Kirista mai suna Dokas ta mutu. Cikin bakin ciki abokanta suka shirya jikinta domin binnewa, sa’an na suka**

**ajiye ta a daki na sama don yin makokinta tare.**





**Amma abokan Dokas sun ji cewa Bitrus yana nan a angwan. Sai suka kira Bitrus ya zo Joffa ban da batan lokaci. Sa’ad da ya zo wurin dakin sama, gwaurayen suka nuna masa zanuwa da rigunan da Dokas ta yi musu. Kowa yana kuka.**

Amma Bitrus ya fitar da su duka waje, sai ya durkusa ya yi addu’a. Yana juya ga jikin, sai ya ce, “Dokas, tashi.” Sai ta bude idanunta, sa’ad da ta ga Bitrus, sai ta tashi ta zauna.





**Sa’an na ya mika mata hannunsa ya daga ta sama; sa’ad da ya kira ga tsarkaku (Kirista) da gwaurayen, sai ya mika ta rayyaye.  Sai ko’ina aka sani a Joffa, kuma mutane da yawa suka ba da gaskiya ga Ubangiji.**

**Bitrus ya zauna na tsawon lokaci a Joffaa gidan da ke bakin teku. Wata rana Bitrus ya haura gida na sama domin ya yi addu’a.**



**Da a ce ya duba a katanga na birnin,**

**da ya ga wadansu masu tafiya suna zuwa nemansa.**

**Wadannan maza ‘yan hidimar wani babban sojan Romawa mai suna Koneliyus wanda yake wa Allah sujada.**



Koneliyus ya aike ‘yan hidimarsa domin su nemi Bitrus saboda mala’ika ya gaya masa a cikin ru’uya cewa, “Ka aika a kira Bitrus.  Yana kwana a gidan Simiyon,



mai gyaran fatu wanda gidansa yana bakin teku. Zai gaya maka abin da lallai sai ka yi.”

**Yayinda Bitrus yana addu’a a gidan sama, Allah ya aiko masa da ru’uya. Ya ga kamar ana saukar da wani babban kwano ne zuwa kasa. A cikin kwanon akwai dabbobi da tsuntsaye.**



**Bitrus ya sani tabas irin abubuwan da suke a ciki “marar tsarki” ne.  Wannan yana nufi cewa duk mai addinin Yahudawa bai kamata ya ci irin su ba. Nan da nan, wata murya ta zo gareshi. “Tashi, Bitrus, ka kashe ka ci.”**



**“Ba haka ba, Ubangiji!” Bitrus ya gaya wa Allah. “Ban taba cin wani abu banza ko marar tsabta ba.” Muryar ta sake yi masa magana sau na biyu. “Duk abin da Allah ya tsabtace, dole ba za kira shi banza ba.” An yi haka sau uku. Sa’an nan an dauke kwanon zuwa sama.**



Bitrus bai gane manufar ru’uyar ba.  Yayinda yake tunani game da shi, Allah ya gaya masa cewa mutane uku suna nemansa kuma sai ya bi su. Sa’ad da mutane ukun nan suka gaya wa Bitrus cewa mala’ika mai tsarki ya gaya wa Koneliyus ya kira shi, sai Bitrus ya gane cewa Allah yana kai shi wani wuri ne.  Washegari, da shi da abokansa shida suka tafi gidan Koneliyus.







**Watakila, yayinda ya fara tafiya zuwa gidan mutumin da ba Bayahudiya ba, sai Bitrus ya far gane cewa Allah yana kaunar wdanda ba Yahudawa ba – cewa Allah yana so duka al’ummai su sani Yesu shi ne Mai Ceton duniya.  Sa’ad da Bitrus ya aki gidan, Koneliyus ya fadi kasa cikin sujada a gabansa.**

“Tashi tsaye.  Ni ma da kaina ni mutum ne,” Bitrus ya gaya wa Koneliyus.  Sa’an nan ya ce wa duka mutanen da suke a gidan, “Kun san yadda karya doka ne idan mutumin Yahuda ya yi cudanya ko ya je wurin wani wanda shi daga wani al’umma ne.” “Amma Allah ya riga ya nuna mini cewa kada in kira wani banza ko marar tsabta.”



**Bitrus ya gaya wa wadannan 'Yan Al'ummai (wadanda ba Yahudawa ba) cewa Yesu shi ne dan Allah wanda ya mutu a kan giviye ya kuma tashi daga mutuwa don ya zama Mai Ceton duniya.  Sa'an nan Ruhu Mai Tsarki ya fado a kansu sai suka fara rera wakokin yabo ga Allah.**



**Abokan Bitrus guda shida Yahudawa suka yi mamaki. Ya zama kamar ranr Fentikos. Kyautan Ruhu Mai Tsarki ma zub da shi a kan ‘Yan Al’ummai su ma. Sai Bitrus ya yi wa sabobin tuba ga Yesu baftisma.**



**A Urushalima, Kiristoci sun yi wa Bitrus fada domin ya ziyarci ‘Yan Al’ummai. Sai Bitrus ya gaya musu ru’uyar daya gani da kuma na Koneliyus wanda ya karba a cikin addu’a. Sa’ad da suka ji wadannan abubuwa, Kiristocin Urushalima suka yi shuru. Sai suka daukaka Allah, wanda, ta wurin addu’a, ya nuna wa ikkilisiya Kirista cewa kaunar Allah yana nan ga kowa da kowa.**



**Bitrus da Ikon Addu'a**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Ayyukan Manzani 9-12**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**